


Matakan Samun Karɓuwa

Yesu ya ɗauki ƙiyayyar mu domin mu sami karɓuwar Sa a wurin Uba



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Akwai matakai huɗu da dole ka ɗauka domin ka sami karɓuwa a wurin Allah. Abu na farko shi ne ka gafarta wa duk wanda ya ƙi ka ko ya cutar da kai ta kowace hanya. Kamar yadda Yesu ya umurce mu:

> "Ko yaushe kuka tsaya yin addu'a, in akwai wanda kuke jin haushinsa, ku yafe masa, domin Ubanku da yake cikin sama shi ma ya yafe muku laifofinku" (Markus 11:25)

Wannan magana ta ƙunshi komai: idan ka riƙe wani abu game da wani, ka gafarta, daga nan Allah ma zai gafarta maka. Amma idan ba ka gafarta wa waɗansu ba, Allah ba zai gafarta maka ba. Wannan gaskiyar ta shafi musamman halayyarmu ga iyayen mu, waɗanda galibi ke haifar da matsalar ƙiyayya. Rayuwar wasu ta canza lokacin da suka fahimci cewa suna da wani haƙƙi daga Littafi Mai Tsarki na girmama iyayen su. Afisawa 6:2 ta ce:

> "'Ka girmama mahaifinka da mahaifiyarka,' wanda shi ne umurni na farko mai alƙawari."

Wannan ba yana nufin cewa ka yi watsi da kurakuransu gaba ɗaya ba, amma dole ne ka gafarta masu kuma ka ƙudura za ka girmama su gwargwadon iyawar ka. Ban taba ganin wanda ke da dangantaka marar kyau da iyayensa kuma ya kasance mai albarka da wadata ba. Na biyu, dole ne ka watsar da mummunan sakamakon ƙiyayya: ɗaci, fushi, ƙiyayya, tawaye. Waɗannan halaye guba ne; za su shafi dukan rayuwar ka. Za su haifar da manyan matsaloli na tunani, har ma da matsalolin jiki. Bai kamata ka riƙe waɗannan tunane tunanen ba.

Ta wurin yanke shawara mai ƙarfi da yardar ka, ka ture su daga gare ka. Ka fadi da tabbaci, "Na kawar da ɗaci, fushi, ƙiyayya, da tawaye." Mutane da suka tuba daga shan giya sau da yawa ana gaya masu, "Fushi kaya ne da ba za ka iya ɗauka ba." Wannan gaskiya ne. Babu wani daga cikin mu da zai iya kasaancewa da fushi. Illolinsa suna da guba.

Na gode maka, Yesu, saboda aiki ka a kan gicciye. Ina gafarta wa duk wanda ya ƙi ni, kuma na kawar da ɗacin rai,

© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

fushi, ƙiyayya, da tawaye. Ina furta cewa Yesu ya ɗauki ƙiyayya ta domin in sami amincewar Sa a wurin Uba. Amin.

Abincin Yini ★

Kwafi: WD-B097-145-HAU

Sabuntawa ta ƙarshe: 24 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources



© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.